# Wanda yake son Allah Ya tseratar da shi daga baƙin cikin ranar Alƙiyama, to, ya yaye wa wanda yake cikin wani mawuyacin hali, ko ya sarayar masa (wani haƙƙi ko nauyin da ya ke kansa)

Daga Abu Katada - Allah Ya yarda da shi - cewa shi ya nemi wani wanda yake bin sa bashi, sai ya ɓuya daga gare shi, sai ya ce: Lallai ni bani da kuɗi, sai ya ce: (tskaninka da) Allah? ya ce: (tsakanina da) Allah? ya ce: Lallai ni naji Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana cewa: "Wanda yake son Allah Ya tseratar da shi daga baƙin cikin ranar Alƙiyama, to, ya yaye wa wanda yake cikin wani mawuyacin hali, ko ya sarayar masa (wani haƙƙi ko nauyin da ya ke kansa)".
[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Abu Katadah alAnsari - Allah Ya yarda da shi - ya kasance yana binciken wani wanda yake binsa bashi wanda yake ɓoye masa, sai ya same shi, sai wanda ake bi bashi ya ce: Lallai ni bani da kuɗi, kuma bani da dukiyar da zan biya bashinka. Sai Abu Katadah - Allah Ya yarda da shi - ya sa ya rantse da Allah cewa shi bashi da dukiya? Sai ya rantse da Allah cewa shi mai gaskiya a abinda yake faɗa. Sai Abu Katadah - Allah Ya yarda da shi - ya ce lallai shi ya ji Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana cewa: Wanda yake so kuma yake farin ciki Allah Ya tseratar da shi daga baƙin cikin ranar alƙiyama da tsanace-tsanancanta da tsorace-tsoracenta, to ya yayewa wanda yake cikin ƙunci, shi ne cewa ya ƙara (lokaci) ya jinkirta neman bashin, ko ya sarayar da sashin bashin ko ma dukkansa.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee